Duk abinda mai yawansa yake sa maye to kaɗan ɗinsa haramun ne

Daga Jabir ɗan Abbdullahi - Allah Ya ƙara yarda a gare su - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Duk abinda mai yawansa yake sa maye to kaɗan ɗinsa haramun ne".

[Hasan ne] [Abu Dawud da Tirmizi da Ibnu Majah da Ahmad ne Suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bayyana cewa dukkan abin sha ko abin ci da yake kawar da hankali lokacin da aka ci ko aka sha mai yawa daga gare shi, to cin kaɗan daga gare shi abin haramtawa ne koda bai tafiyar da hankali ba.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/66036